**Réseau National des Chambres d'Agriculture du Niger (RECA) et partenaires**

Mars 2018

# Tsutsar masara da ake cema da turanci : *Spodoptera frugiperda*

A shekara ta 2016, wata sabuwar tsutsa ta bayana a kasar africa,wanan tsutsar ta mamaye kasashen africa da dama kamar su nigeria,benin,togo,africa ta kudu da sauran su ; tsutsar masara spodoptera frugiperda tayi banna sosai a cikin gonankan masara.



Wannan tsutsar masara ana ce mata spodoptera frugiperda a turance,an ganota ne a karon farko jikin masara a garin torrodi da maradi shekara ta 2016 ;tun daga wanan lokaci sai ta bazu a dukan fadin kasa.

Abun al'ajabi wanan tsutsar bata tsaya ga masara kadai ba, a lokacin daminar bara a garin maradi da torodi ta apkama gonankan hatsi inda tayi bana sosai ;wanan tsutsa dai babbar matsala ce ga hatsi da dawa, ya kamata manoma su nemi saninta don su yaketa.

## 1. Yaya ake gane tsutsar masara ?

Da farko dai ya kamata manomi yasan cewa ita dai tsutsa ita ce jinjirar malam batata. Wato ita ke rikidewa ta zama malam batata babba wanda ke iya aihuwa kuma ya tashi aman tsutsar kadai ke yin banna.



Tsutsar masara nada wasu zane toka toka a dukan jikin ta ;

Tsutsar nada wani zane kamar magamar hanya daga tsakiyar kanta ;

A aji na karshen tsutsar ta girma tsawon ta ya kai 3cm ;

Tsutsar nada launi daban daban,kama daga masara,duhu duhu da baki,launin duhun yahi yawa ;

| | | |
|---|---|---|
|  |  |  |
| Launi daban daban na tsutsa a aji na farko | | |

## 2. Yaya ake gane bannar da tsutsar tayi ?

- Tsutsar na kama shipkar ta masara ga baki daya tun daga kara,kununwa ,hure da goyo ;
- Lokacin da bannar tayi tsanani kunnuwan masarar duka sai su huhude kamar fara ta bi ta huce ;
- In ba an bude ganyen masara ba za a iya ganin  tsutsar  ba saboda a nan ne take buya wani lokaci kuma a cikin hure kahin ya bude.

| | |
|---|---|
|  |  |
| Kunuwan masara da tsutsar ta huhude | Yadda aka bude ganyen masara don ganin inda tsutsar ta buya |

- Tsakanin gayen ana iya ganin wani bilbidi mai launin duhu duhu alamun tsutsar.
- In bannar tayi lati tsutsar na boyewa cikin kunshin masarar sai ta rinka cin diyan.

| | |
|---|---|
|  |  |
| Tsutsa kewaye da kashinta (bilbidin) | Tsutsa kwonce jikin goyon masara |

- In bannar tayi tsanani tsutsar na cinye dukan kwayoyin masara, koda an girbe za a samu goyo da dama da basu da diya hakan kuma na kawo asarar albarkatun noman ; yawan bannar ya danganta ne da yawan diyan da maccen malam batata ke aihuwa domin cikakiyar maccen malam batata na iya  saka hiye da kwai dubu tsawon rayuwa ta (kamar yadda masana suka bayana).

|  |  |
|---|---|
| Bannar  tsutsar jikin sabon dashe,kananan hudodi saman tohon | Banna jikin goyon masara |

Manoma kuyi hattara,ba kowane  hudodi ne ke nuna cewar akoye tsutsar masara a cikin gonar ku ba,akoye wasu miyagun kwari dake irin wanan bannar aman illar su bata kai ta tsutsar masara ba,kenan manoma  ayi kokarin gano tsutsar don a yaketa.

### 3. Daga ina tsutsar masar ta huto kuma a ina ake samun ta a jamhuriyyar nijar ?

- Halita ce mai saukin yaduwa kuma ta samo asali ne daga(America ta kudu da ta arewa).
- Ta iso kuducin nageria a wata january na 2016
- Daga nan kuma ta isa arewacin benin da togo a watan augusta na 2016, sanan aka gano ta nijar a watan November 2016.
- Malam batatan na iya tahiya mai tsawo har ya kai nisan kilometer 2000 musaman ma lokacin iska tunda iskan ke karamishi karhi tahiya
- A yau tsutsar masara ta mamaye dukan jahohin kasa banda jahar diffa inda har yanzu ba’a gano ta ba.

Tsutsar masara babbar matsala ce ga mahiman abincin da muke nomawa cewa da hasti dawa da sauran su kenan ya kamata mu yaketa.

### 4. Wanne irin hanyoyin suka dace mu bi don yakar tsutar masara ?

Babbar matsalar ita ce,yaki da wanan stutsar nada matukar wahala domin malam batatan da ke haifuwar wannan tsutsar tashi yake,gashi kuma da yawan aihuwa cikin

kakanan lokaci, sanan kuma tsutsar da yake aifowa na cin shipkoki da dama,sanan kuma yana saukin bijirema magani.

- In gonar ku ta taba haduwa da stustar masara to abu mafi kew shine kada ku shipka masara sai bayan wani lokaci,in kuma bakuda wata dubara to da zarar shipkar ta fara girma to sai kuyi kokarin saka maganin da aka hada da tanshi ko( taba)wanda keda saukin hadawa ; ,wanan magugunan na sa malan batatan dake aifuwar stustar ya nisanci shipkokin kenan baya samun damar yin kwayayen.

- In tsutsar ta shiga gonar ku to sai ku zuba magugunan da ke kumshe da sinadirai kamar su Acetamipride, Indoxacarbe ou Emamectine.

- Ku kiyaye zuba magani iri guda har sau uku a cikin gona,ku rinka gawraya maguguna saboda zuba magani guda na iya sa tsutsar ta saba da shi har ta kai ga bijire mishi kenan maganin baiyi unfani ba.

- Manoma kuyi hattara akoye magani da ake cema Lambdacyhalothrine(konko da kolba masu launi ruwan hoda),ko kuma pia pia to wanan basuda karhi wajan yaki da stutar masara .

Idan kuna bukatar Karin bayani to sai ku tuntubi mashawartan nan na kugiyoyin **RECA** da **CRA** kan **92 24 24 24** (Orange) ; **89 97 97 74** (Airtel**)** ;
**84 74 74 74** (Moov) ; **93 32 38 92** (Niger-telecom) ;
Ko kuma whatsapp a kan **92 24 24 24** (Orange) ko kuma a kan **89 97 97 74** (Airtel).

Wanan layoyin dai kungiyoyin **RECA** da **CRA** ne suka tanadar muku su don waye muku kai kan ayyukan ku na noman gandari.

---

*Cette note est la traduction d'une note technique préparée par des techniciens du Réseau National des Chambres d'Agriculture (RECA), de l'Institut National de la Recherche Agronomique et de la Chambre Régionale d'Agriculture de Tillabéri. Elle a été réalisée avec l'appui financier du Projet d'Appui à l'Agriculture Sensible aux Risques Climatiques (PASEC).*